# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Kowa dabam Allah ya yi shi: Mutunta haƙƙin tsirarru
## Kashi na shida: Kyamar baƙin haure a ƙasar Afirka ta Kudu

Wadda ta rubuta: Leonie March
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**'Yan Wasa:**

Mai ba da labari

Marie: 'yar shekara 30

Baruti Amisi: ɗan shekara 45

Jahmil Qubeka: ɗan shekara 30

Wasu mutane

**Mai gabatarwa:**

Masu saurarenmu, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin kashi na shida na shirinmu na "Ji Ka Karu" a kan mutunta haƙƙin mutane tsirarru a Afirka. A shirin namu na yau za mu mayar da hankali ne a kan wata matsala mai sarƙaƙiya ta tsoro da kuma ƙyamar da ake nuna wa baƙin haure a ƙasar Afirka ta Kudu. Abin da ake nufi a nan shi ne, yadda mutane suke jin tsoro da kuma ƙyamar baƙin haure ba tare da wani dalili ba. Shi dai irin wannan tsoro da mutane kan ji, ba inda babu shi a faɗin duniyar nan. Don haka abin ba wai ƙasar Afirka ta Kudu kaɗai ya ta'allaƙa ba. Sai dai kuma a 'yan shekarun da suka wuce irin mugun farmakin da ake kai wa baƙin haure a wannan yanki na kudancin Afirka ya daɗa ƙaruwa. Abin takaici shi ne ganin yadda rayuwar baƙin haure, musamman ma dai waɗanda suka fito daga ƙasashen Afirka, a ƙasar ta Afirka ta Kudu ke shiga cikin haɗari da kuma mawuyacin hali. Sai dai kuma akwai wani yunƙuri da ake yi domin ganin an yi riga-kafin ɓarkewar tashin hankali. Haka kuma wannan yunƙuri da ake yi yana samun nasara.

**Mai ba da labari:**

Yanzu dai ga mu a cikin garin Durban inda ake iya jin hayaniya ta yau da kullum. Ga dai motocin tasi nan suna ta hon don neman fasinja, ga mutane masu yawa nan suna ta tsallaka titi, gefen hanyoyin kuma cike yake da ƙananan tebura inda mata ke yin kasuwanci. Suna sayar da komai da komai, tun daga kan'ya'yan itatuwa, da katin waya, da kuma robobi. Ni da na hanga ban ga alamun Marie ta fita dabam daga sauran mutane ba. Ga ta nan dai tana tura jaririyarta a cikin keken jarirai, tana sanye da riga mai ruwan hoda, da kuma dogon siket fari. Amma kuma fa wannan mata mai suna Marie wadda 'yar shekara 36 ce 'yar gudun hijira ce daga Jamhuriyar Dimukuraɗiyyar Congo. Ta bayyana mini cewa, a ko da yaushe 'yan gari kan nuna mata cewa ita fa baƙuwar haure ce, don haka ba sa maraba da ita.

**Bayanin Marie:**

*"Allah dai Ya ƙaddara zamanmu ne a nan ƙasar ta Afirka ta Kudu, amma 'yan ƙasar ba sa ƙaunarmu. Ko da yaushe sai ka ji sun ce, "Hey, Makwerekwere!"*

*Idan ka je kasuwa ba ka iya yarensu ba, to kana cikin matsala. Idan sun tashi yi maka magana sai su yi da yarensu, idan ba ka fahimci abin da suka ce ba, sai su kore ka suna ce maka, "Hamba, Makwerekwere!"."*

**Mai ba da labari:**

Wannan kalma ta "Makwerekwere" kalmar nuna ɓatanci ce da 'yan Afirka ta Kudu kan yi amfani da ita don muzguna wa baƙin haure, musamman ma dai 'yan gudun hijira na ƙasashen Afirka. Wannan abu ya jawo mummunan tashin hankali cikin shekara ta 2008 wanda ya jawo kai farmakin ƙyama a garuruwan ƙasar. Waɗannan garuruwa dai su ne inda aka tilasta wa baƙaƙen fata zama a lokacin da ake mulkin nuna wariyar launin fata. A ko'ina a faɗin ƙasar akan tare 'yan gudun hijira a doke su ko ma a ƙone su. Wasu kuma a ji musu raunuka, sannan kuma a fasa kantunansu, a ɗebe musu dukiyoyinsu, kana kuma a lalata musu gidaje.

**Bayanin Marie:**

*"Sukan kira mutum su ce, "Kai baƙon haure, me ka zo yi a ƙasarmu? Zo ka koma ƙasarku." Suna iya cin mutuncin mutum nan take. Kuma za su iya yi maka duk abin da suka ga dama. A wannan lokacin mukan gudu cikin coci ne mu nemi mafaka. Haka muka yi ta yi har na tsawon watanni biyu zuwa uku, muna ɓuya a cikin coci ba tare da mun fito waje ba. Fasto ɗin cikin cocin ne ma yake kai mana abinci can. 'Ya'yanmu ba sa zuwa makaranta har na tsawon watanni uku saboda abin ya yi mummunan ɓaci."*

**Mai ba da labari:**

Abin ma dai ya fi ƙazanta a cikin shekara ta 2008. Sai dai kuma ƙyamar baƙin haure ba wani sabon abu ba ne a lokacin. Kuma har yanzu yana nan a cikin yankunan biranen da talakawa suke da zama. Kamar dai yadda Baruti Amisi ya bayyana mana. Shi ma dai ya zo ƙasar Afirka ta Kudu ne daga Jamhuriyar Dimukuraɗiyyar Congo a matsayin ɗan gudun hijira. Yanzu kuma yana aiki ne a matsayin malamin jami'a mai gudanar da bincike a jami'ar Kwazulu Natal.

**Bayanin Baruti Amisi:**

*“Na zo ƙasar Afirka ta Kudu ne tun shekarar 1997. Mun ga kyasa-kyasai na ƙyamar baƙin haure. Na ga yadda aka dinga sukan mutane da wuƙa saboda kawai ba sa iya magana da yaren mutanen garin, kuma na ga mutanen da aka kashe saboda wannan dalili. A yammacin garin Cape Town na ga yadda aka dinga kashe mutane ana yanka su gunduwa-gunduwa. Wannan shi ne fa irin abin da fushin mutane zai kai su ga aikatawa. Suna kashe mutane kuma suna yanka su gunduwa-gunduwa. Amma fa wannan abu ne da ya faru kafin shekara ta 2008.”*

**Mai ba da labari:**

Tabbas ba kowane ɗan Afirka ta Kudu ne ke ƙyamar baƙin haure ba. Da yawa daga cikinsu ma kan kawo ɗauki idan tashin hankalin ya kai maƙura. Wasu kuma, kamar mai yin fina-finan nan mai suna Jahmil Qubeka, sai suka fara fitowa fili a shekara ta 2008, suna nuna adawarsu da irin wannan ƙyama da ake wa baƙin haure.

**Bayanin Jahmil Qubeka:**

*“A wannan lokacin na yi takaicin kasancewata ɗan ƙasar Afirka ta Kudu. Sai nake jin kamar na ce, “Allah Ya kiyaye, amma mu dai ba da yawunmu ake yin haka ba. Kuma ma, me ya sa irin haka take faruwa?” Sam abin akwai ɗaure kai. A matsayinmu na ’yan Afirka ta Kudu a lokacin da ake mulkin wariya, mun samu kanmu a matsayin ’yan gudun hijira a wasu ƙasashen. Amma yanzu ga shi mun kasa haƙurin zama da waɗansu mutanen. Wannan shi ne babban abin da ya fi damuna.”*

**Mai ba da labari:**

Sai dai kuma har yanzu ana cikin halin ɗar-ɗar, musamman ma a manyan biranen ƙasar. Har yanzu ana kai hari kan ’yan gudun hijirar da ke zuwa daga ƙasashen Afirka waɗanda kuma suke fatan samun kyakkyawar rayuwa. Yawancin fafutukar da ake yi ta neman ayyukan yi da gidajen zama, ita take haddasa wannan tashin hankali a waɗannan yankuna na talakawa. Ga bayanin da waɗansu ’yan ƙasar ta Afirka ta Kudu su uku suka yi game da yadda

mutane suke ganin wannan al'amari.

**Bayanin wasu mutane:**

***Muryar wata mace:***

*"Muna samun matsala da waɗannan baƙin hauren. Sam ba sa taimaka wa tattalin arziƙin Afirka ta Kudu ya bunƙasa. Sai dai kawai su kwashe komai su tafi abinsu."*

***Muryar wani matashi:***

*"Ran mutane duk a ɓace yake. Domin kuwa za su iya yin kisa don su mallaki gida."*

***Muryar wata mace:***

*"Mu ba ma son zamansu a nan. Kasar Afirka ta Kudu ta 'yan Afirka ta Kudu ce kaɗai. Mu muka yi yaƙi wajen ƙwato 'yancin wannan ƙasa, don haka yanzu tamu ce. Kuma 'yancin namu ne."*

**Mai ba da labari:**

Sai dai kuma an samu akasi, domin kuwa wannan 'yanci da suke magana a kai, shi ne ke jawo sauran 'yan ƙasashen Afirka matalauta da kuma waɗanda ake rikici a ƙasashensu zuwa Afirka ta Kudun. Kiyasin da aka yi na 'yan gudun hijira masu izinin zama da marasa izini ya kai kimanin miliyan uku zuwa huɗu. Dubun dubatar mutanen da suka gudu daga yankunan da ake nuna ƙyama ga baƙin haure a shekarar 2008, har yanzu suna zaune a cikin majami'u da kuma sauran matsugunai inda suke cike da tsoron komawa yankunan da suke da zama a cikin gari.
Amma kuma ko a cikin biranen ma ƙyamar baƙin haure ta zamo ruwan dare. Baruti Amisi wanda malamin jami'a ne mai yin bincike, wanda kuma shi ne shugaban Kungiyar 'Yan Gudun Hijira ta Kwazulu Natal, ya sha jin irin waɗannan labaran na cin zarafi da nuna wariya.

**Bayanin Baruti Amisi:**

*"Akwai masu gidajen da suke ganin za su iya ba da gidajensu haya ga*

*waɗanda ma ba 'yan Afirka ta Kudu ba. Dalili kawai shi ne, 'yan hayar ba za su dame su da maganar gyara ba, idan kuwa suka yi za a iya yi musu barazanar kora saboda ba su san haƙƙinsu ba. Ba wata wahala a ci mutuncinsu domin kuwa babu wanda ya damu da su. Idan yanzu na kira 'yan sanda, ba za su zo ba sai gobe saboda kawai sun ji irin karin harshena. Ba a karɓar 'ya'yanmu a makarantu saboda ana tsammanin ba za mu iya biyan kuɗin makaranta ba. Mata 'yan gudun hijira na fuskantar baƙar wahala a yayin da suka zo haihuwa saboda kawai su ba 'yan Afirka ta Kudu ba ne. Zan iya lissafa maka nau'in ƙyama dabam-dabam da ake nuna mana a nan ƙasar. Abin zai ba ka mamaki."*

**Mai ba da labari:**

Wannan ƙiyayya da ake nuna wa baƙin haure ta bazu har zuwa majami'u, kamar dai yadda Marie ta bayyana mana, a lokacin tana riƙe da ɗanta yana wasa a kan cinyarta. Marie dai mai bin addinin Kirista ce, kuma kamar sauran abokanta 'yan ƙasar Congo tana zuwa majami'ar Charismatic ce da ke garin Durban. Wannan majami'a tana bayar da taimako ne da kuma matsuguni ga 'yan gudun hijirar da ke cikin tashin hankali. Marie ta kaɗu sosai a lokacin da ta ji wani fada na Coci yana yin huɗubar a nuna ƙyama ga baƙin haure.

**Bayanin Marie:**

*"Abin mamaki! Wai fa wannan fada ne, ya kuma san duk muna wurin, amma duk da haka yake cewa: "Mun gaji da zaman wannan baƙin hauren. Dole ne su koma ƙasarsu. Sun zo sun ƙwace mana ayyukanmu, suna ƙwace mana 'ya'yanmu suna aurewa." Duk fa a bainar jama'a yake faɗin haka, kuma shi fa fada ne na babbar majami'a, yana yi wa mutane huɗubar yadda za su yi maganin baƙin haure. Wannan ne ya sa muke cewa mutanen ƙasar nan ba za su taɓa ƙaunarmu ba."*

**Mai ba da labari:**

Mayar da hankali ga irin ƙalubalen da talakawa 'yan Afirka ta Kudu da ma baƙin haure suke fuskanta na rayuwa, abu ne da zai amfanar. Kamar dai yadda Baruti Amisi cikin murmushi ya yi mana bayani.

**Bayanin Buriti Amisi:**

*"Mun samu damar kare fitinar da ƙyamar baƙin haure ka iya kawowa a cikin garuruwan da talakawa suke da zama. Mun samu damar yin haka a yankuna da dama. Don haka aikinmu yana tasiri."*

**Mai gabatarwa :**

Masu saurare, muna fata kun ji daɗin wannan shiri namu na "Ji Ka Karu" na yau a kan irin bambancin da ake nuna wa 'yan gudun hijira a ƙasar Afirka ta Kudu. Wakiliyarmu da ta kawo mana wannan rahoto a cikin wannan shiri ita ce Leonie March. Idan kuna neman ƙarin bayani ko kuma kuna son sake jin wannan shiri na yau, ko kuma sauran shirye-shiryenmu da suka gabata, sai ku ziyarci adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe. Za ku kuma iya aiko mana da ra'ayoyinku a shafinmu na 'Facebook'. Ku kasance lafiya.